## Simon Ockley

*(1678-1720) Professor na Larabci a Jami'an Cambridge.*

- "Wani abu daya kamata a lura da shi shine Mahaifiyarshi ta haife shi a Mecca, a dakin Ka'ba ; wanda bai taba faruwa da wani ba."
  [*History of the Saracens*, London, 1894, p. 331]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Washington Irving

*(1783-1859) Sananne a zaman "Baamerike na farko marubuci".*

- "Yana daga cikin mafifici acikin ficaccen jinsi na Koreish. Yana da kyawawan siffofi da ake karramawa a Larabawa: zuciya, iya magana, da yawan kyauta. Yanayin kwarjininshi ya sama mishi daga annabi lakanin Zakin Allah, wasu daga cikin kyawun zancen shi da maganganunshi na tsare a wajen Larabawa; kuma kyautanshi ya bayyana wajen rabiya tskanin wasu, kowani juma'a, abun daya saura a baitulmali. Game da alfarman shi, mun bada misalai da dama; irin kyamatar kowani karya da kaskanci, da kuma rashin nuna son kai a duk halin da yake ciki."
  [*Lives of the Successors of Mahomet*, London, 1850, p. 165]

- "Yana daga cikin na karshe kuma masu mutunci a Musulman farko, wanda ya koyi kishin addini daga kusantan Annabi da kanshi, yabi har zuwa karshe saukin misalansa. Ana ambaton girmama shi azaman kalifa wanda ya bada kariya ga Kyawun Rubutu. Ya kan tsunduma a tsara kasidu , kuma an kare mafi yawn fadin shi da karin magana daga bata, an kuma fassara zuwa yarurruka da dama. Tambari da rubutun: 'Masarautan na Allah ne'. Daya daga cikin fadin shi yana nuna yadda bai dauki ababen wannan duniyan gidan wucewa komai ba, 'Rayuwa ba wani abu bane face inuwan gajimare – mafarkin mai bacci'."
  [*Lives of the Successors of Mahomet*, London, 1850, pp. 187-8]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Robert Durey Osborn

*(1835-1889) Major da Bengal Staff Corps.*

- "Tare da shi mafi gaskiyan zuciya da mafi kyawun Moslem wanda tarihin addinin Mohammad ya kare don tunawa da shi."
  [*Islam Under the Arabs*, 1876, p. 120]

**In ana son karin bayai kan Imam 'Ali bin Abi Talib, ziyarci:**

***http://al-islam.org/faq/***

*v1.0*

*Haka Allah yake nuna muku ayoyin shi ko za ku hankalta*
(Qur'an 2:242)

# Me Wa'yanda ba Musulmai ba ke cewa kan ...

# 'Ali

MAGAJIN ANNABI MUHAMMAD NA FARKO
*(Aminci da Albarka su tabbata a gare su )*

Imam 'Ali bin Abi Talib ne magajin Annabi Muhammad, amincin Allah ya tabbata a gare su. Wannan tarin gajerun bayanai da aka nakalto daga sanannun mutanen wasu addinai, wanda suka kunshi malamai, marubuta, 'yan falsafa, masu kasida, 'yan siyasa, da masu gwagwarmaya.

## Thomas Carlyle

*(1795-1881 Marubucin tarihi a scotland, mai zargi, da rubutu kan zamantakewa .*

- "Game da Ali yana karami, ba wanda zai san shi ba face ya so shi. Halitta mai daukaka na hali, yadda ya nuna kansa, a yanzu da kuma ko da yaushe nan gaba; cike da tausayawa, da rashin tsoro. Ya kasance gwarzo ; jarumtaka kaman na zaki; duk da haka ga kamala, gaskiya da kulawa da ya dace da Jaruman Nasara."

  [*On Heroes, Hero-Worship, And The Heroic In History*, 1841, Lecture 2: The Hero as Prophet. Mahomet: Islam., May 8, 1840)]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Edward Gibbon

*(1737-1794) Ana daukanshi a zaman babban masanin tarihin zamanin shi.*

- " Ba wani mai hidima ma addini daya kai kishi da karaman Ali. Ya tattara iyawan mai kasida , soja, da kuma bawan Allah; hikimansa har yanzu yana numfasawa a tarin zantukan halaye da addini; kuma kowani makiyi, in su ka gamu da baka ko da takobi, za aci galaba a kanshi da furuci ko gwarzantaka. Daga farkon aikin shi zuwa ayyukan karshe na jana'izan shi, bai taba barin Annabi ba, wanda ke farin cikin kiran shi kani, magajin shi, da kuma Haruna mai da'a ga Musa na biyu."

  [*The Decline and Fall of the Roman Empire*, London, 1911, volume 5, pp. 381-2]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Philip Khuri Hitti

*(1886-1978) Farfesa na Yarurrukan Semites a Princeton University*

- "Jarumi wajen yaki, mai hikima wajen shawara, kaifin basira, gaskiya ka abokanshi, alfarma ga makiyanshi, ya zama abun kaikwayo na kamala da jarumtan Musulmai (*futuwah*) da Sulemanun tarihin Larabawa, kewaye da sunanshi akwai kasidu, karin magana, wa'azozi da labarai wanda basu irguwa suke tattare."

  [*History of the Arabs*, London, 1964, p. 183]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Sir William Muir

*(1819 - 1905) Dattijo da masani a Scotland. Ya rike matsayin Sakatare na Waje da gwamnatin India da kuma Leftana gwamna na Kasashen Arewa maso Yamma.*

- "Yana da kaifin basira, mai tausayi, da kuma kusantakan aboka, ya sadukar da kanshi ga Annabi zuciya da ruhi tun yana yaro. Saukin kai, mai shiru, ba shi da buri, lokacin daya samu mulkin rabin kasashen Musulmai, an lankaya masa ne sabanin ya nema."

  [*The Life of Mahomet*, London, 1877, p. 250]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Dr. Henry Stubbe

*(1632-1676) Classicist, polemicist, physician, and philosopher.*

- "Yana da kin duniya, haskenta da kyale-kyalenta, ya ji tsoron Allah matuka, ya ba da sadaka, adali ne a dukkan ayyukanshi, kankan da kai da saukin kai; yana da kai fi hankali da fasahan da babu shi, ya nada ilimi mai yawa, ba a kimiya da ke kare wa a baki ba amma yana gudana a aikace."

  [*An Account of the Rise and Progress of Mahometanism*, 1705, p. 83]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Gerald de Gaury

*(1897 - 1984) A distinguished soldier and diplomat.*

- "Ya kasance mai hikima a shawarwari kuma jarumi a wajen yaki, ya na mutunta abokantaka da kuma alfarma wa makiya. Zai kasance har abada na gaba a jarumtaka da daukaka na Musulunci."

  [*Rulers of Mecca*, London, 1951, p. 49]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Wilferd Madelung

*Alaramman Larabci a Jami'an Oxford*

- "A lokacin da aka fuskanci karyan gadara na Umayya a kan halattacciyar mulki na Musulunci a zaman Kalifan Allah a kasa , da kuma ha'inci na Umayya , gwamnati mai sabani da rarraba kai, da ramakon gayya, sun zo sun fahimci gaskiyan shi, tsayayyar kishinsa na daukakar Islam, zurfin biyayya ga abun da yasa gaba, yadda yake kula da dukkan mabiyan shi ba nuna banbanci, da kuma alfarma gafartawa makiyan shi da yayi galaba akan su."

  [*The succession to Muhammad: a study of the early caliphate*, Cambridge, 1997, pp. 309-310]

✶ ✶ ✶ ✶ ✶

## Charles Mills

*(1788 - 1826) Nagaba wajen rubutun tarihi a lokacinsa.*

- "A zaman shugaban gidan Hashem da kuma kani kuma sirikin wanda Larabawa ke girmamawa …, abun alwashi ne ace Ali bai samu Kalifa dai dai bayan rasuwan Mohammad ba. Tari da gatn haihuwa da aure ga karin abokantan shi da Annabi. Dan Abu Talib na daga farko cikin wanda suka fara musulunta ga kuma sanannen fadin Mohammad cewa game da shi Harunan Musa na biyu ne. Baiwan shi na balaga da tsananin rashin tsoro a zaman jarumi, na godiya ma kasan da a hukuncin ta yin zuciya halin kwarai ne kuma balaga hikima ne."

  [*An history of Muhammedanism*, London, 1818, p. 89]